# GOD'S SIMPLE PLAN OF SALVATION

## Introduction

I Yahaya 5:13 Na rubuto muku wannan ne, ku da kuka gaskata da sunan Ɗan Allah, domin ku tabbata kuna da rai madawwami.

## I Dukan mu mun yi zunubi. Dukan mu mun yi abubuwan da zasu sa ɓacin zuciya ga Allah. Babu wani ɗaya wanda ya zama marar laifi.

Romawa 3:10 Kamar yadda yake a rubuce cewa, "Babu wani mai adalci, babu, ko ɗaya,

Romawa 3:23 gama 'yan adam duka sun yi zunubi, sun kasa kuma ga ɗaukakar Allah.

Romawa 5:12 To, kamar yadda zunubi ya shigo duniya ta dalilin mutum ɗaya, zunubi kuwa shi ya jawo mutuwa, ta haka mutuwa ta zama gādo ga kowa, don kowa ya yi zunubi.



**We are al sinners!**

## II Tana koyar mana game da abubuwan da zunubi yakan haifar –

Romawa 6:23 "Gama sakamakon zunubi mutuwa ne, amma baiwar Allah ita ce rai madawwami a cikin Almasihu Yesu Ubangijinmu.:

Apocalypse 21:8 "Amma matsorata, da marasa riƙon amana, da masu aikin ƙyama, da masu kisankai, da fasikai, da masu sihiri, da masu bautar gumaka, da kuma duk maƙaryata, duk rabonsu tafkin nan ne mai cin wuta da kibiritu, wanda yake shi ne mutuwa ta biyu."

## III Yesu Kiristi ya mutu dominmu! Mutuwar Yesu ta biya don farashin zunubanmu. Tashin Yesu daga matattu ta gwada cewa Allah ya amshi mutuwar Yesu a matsayin biyarwa don zunubanmu.

Romawa 5:6   Tun muna raunana tukuna, Almasihu ya mutu a daidaitaccen lokaci, domin marasa bin Allah.

Romawa 5:8   Amma kuwa Allah yana tabbatar mana da ƙaunar da yake yi mana, wato tun muna masu zunubi, Almasihu ya mutu dominmu.

Romawa 5:12  To, kamar yadda zunubi ya shigo duniya ta dalilin mutum ɗaya, zunubi kuwa shi ya jawo mutuwa, ta haka mutuwa ta zama gādo ga kowa, don kowa ya yi zunubi.

Romawa 6:23   "Gama sakamakon zunubi mutuwa ne, amma baiwar Allah ita ce rai madawwami a cikin Almasihu Yesu Ubangijinmu.:



**Christ died for sinners!**

# IV   Ba zamu iya ceton kanmu ba.

Actes 4:12    Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk duniyar nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto."

Afisawa 2: 8-9   Domin ta wurin alheri ne aka cece ku saboda bangaskiya, wannan kuwa ba ƙoƙarin kanku ba ne, baiwa ce ta Allah, ba kuwa saboda da aikin lada ba, kada wani ya yi fariya.

Tite 3:5  sai ya cece mu, ba don wani aikin adalci da mu muka yi ba, a'a, sai dai domin jinƙan nan nasa, albarkacin wankan nan na sāke haihuwa, da kuma sabuntawar nan ta Ruhu Mai Tsarki,




**V Saboda mutuwar Yesu a madadinmu, duk abin da ya kamata muyi shine bangaskiya cikinsa, muna amincewa da mutuwarsa a matsayin biya don zunubanmu – kuma zamu sami ceto!**

Romawa 4:24 har saboda mu ma, za a lasafta mana, wato mu da muke gaskatawa da wannan da ya ta da Yesu Ubangijinmu daga matattu,

Romawa 10:9-10,13 Wato, in kai da bakinka ka bayyana yarda, cewa Yesu Ubangiji ne, ka kuma gaskata a zuciyarka Allah ya tashe shi daga matattu, za ka sami ceto. Domin da zuci mutum yake gaskatawa yă sami adalcin Allah, da baki yake shaidawa ya sami ceto. “Duk wanda kuwa ya yi addu'a da sunan Ubangiji zai sami ceto.”

*Idan kana son ka karɓi Yesu Kiristi a matsayin mai cetonka, ga samfurin addu’a anan. Ka tuna, faɗar wace nan addu’a ko wata addu’a dabam ba zai cece ka ba. Amincewa ce kaɗai cikin Kiristi wanda zai iya cece ka daga zunubi. Wace nan addu’a, hanya ce mai sauƙi a furta ga Allah bangaskiyarka a cikin Sa kuma ka gode masa don ya tanadar maka da ceto.*

**”Allah,**

**na sani cewa nayi zunubi gareka kuma na cancanci hukunci. Amma Yesu Kiristi ya ɗauki hukuncin da ya cancance ni, don ta wurin bangaskiya a cikinsa in sami gafartawa. Na juyo daga zunubaina kuma na sa amincewa tawa a cikinka don ceto. Na gode maka don alherinka mai ban mamaki da kuma gafara – kyautar rai madawwami! Amin!”**

**Amazing Grace Publishing * PO Box 1963 * Joshua TX 76058 * 817-426-1828 * E-Mail JamesAV@aol.com**